# YADDA AKE YIN ALWALA A AIKACE



Salla bata yiyuwa saida alwala kuma tilasa alwalar ta zamanto anyi ta da ruwa me tsarki wanda yake bai canja daga asalin kamanninsa na ruwa ba, kamar ruwan kogi ko na rijiya ko na idaniyar ruwa ko na korama.
**A kula da kyau :** komai kankankatar najasa takan lalata ruwan da yake dan kadan, amma idan yana da yawa kamar ya haura lita (210) to najasa bata lalata shi har sai idan ta canja masa kala ko dandano ko kuma kamshi.



**1.** Ana fara alwala da sunan Allah (bisimillah) kuma an so a fara da wanke tafukan hannu a kuma tabbatar sun fita, za ayi hakan sau uku, musamman ga wanda ya farka daga barci
**A kula da kyau :** Ba a son a wanke wata gaba sama da sau uku wannan "MAKARUHI" ne.



**2.** Sannan sai kurkurar baki, tilas ne ayi ta farko, amma idan anyi uku to shi yafi soyuwa kuma yafi falala.
**A kula da kyau :** zuba ruwa a baki da fitar da shi kadai baya wadatarwa, dole ne sai an kurkura shi a cikin bakin. Kuma an so mutum yayi asuwaki yayin kurkurar bakin.



**3.** Sannan sai shaka ruwa a hanci, tilas ne ayi sau daya a kalla, amma idan anyi sau uku shi yafi falala.
**A kula da kyau :** itama shakar hanci bawai kawai za shigar da ruwa hanci bane, dole ne ya zamo ta hanyar shakar ruwa tare da numfashi, kuma ya shiga har cikin hancin sannan a fyato shi ya fito tareda numfashi.



**4.** Sannan sai wanke fuska, itama tilas ne ayi sau daya a kalla, amma idan anyi sau uku shi yafi. Za a wanke ta ne tundaga kunnen dama zuwa na hagu, wannan a kwance kenan, a tsaye kuma tun daga karshe haba har ya zuwa mabubbugar gashin kai.
**A kula da kyau :** Idan gemun mutum yana da yawa to an so ya tsefe shi, amma idan bashi da yawa to tilas ne ya tsefe shi ta yadda ruwa zai ratsa hi.



**5.** Sannan sai wanke hannaye tun daga yan yatsu har zuwa gwiwar hannu tilas ayi na farko amma idan an kara zuwa uku wannan shi yafi.
**A kula :** Ana so a fara da hannun dama kafin ayi na hagu.



**6.** Sannan sai shafar kai baki dayansa, mutum zai shigar da yan yatsunsa guda biyu sabbaba (manuniya) ma kofofin kunnuwansa sannan ya shafi fatun kunnuwansa da manyan yan yatsun nasa (ibhama).
**A kula da kyau :** inda ya wajaba a shafa a kayi shi ne: daga mafarin fuska zuwa keya. Kuma idan gashi yana da yawa ba lalle ne sai an shafi wanda ya sauko ba. Idan kuma babu gashin kwata- kwata to sai a shafi fatar kai kuma tilas ne a shafi fatun kunnwa.



**7.** Sannan sa mutum ya wanke kafafuwansa shima sau daya ne ya wajaba, amma idan akayi sau uku yafi falala.

**FADAKARWA: 1.** Wuraren da ake wankewa a yayin alwala guda hudu ne; **(a)** kurkurar baki da shaka ruwa da wanke fuska **(b)** hannaye **(c)** shafar kai da kunnuwa **(d)** kafafuwa zuwa idan sawu. **2.** Tilas ne a wanke wadannan gabbai a jere daya-bayan -daya, idan kuwa aka bar wata gabar ba a wanke ta ba har jiki ya bushe, to alwala ta baci.
**3.** An so mutum idan ya kammala alwalar ya ce: " **ASH-HADU ANLAIILA'HA ILLALLA'HU WA ANNA MUĤAMMADAN ĂBĐUHU WA RASULU** " "Na shida babu abin bautawa bisa cancanta sai Allah shi kadai yake bashi da abokin tarayya, kuma na shaida annabi muhammadu bawan Allah ne kuma manzonSa ne.